


# MUJALLAR CITAD RADIO
## RADIYON DA ZAKU SAURARA
## www.citad.org/radio

Volume 1, issue 2

**25-09-1442 AH**
**07-05-2021 AD**

***CIBIYAR BUNKASA FASAHAR SADARWA DA CIGABAN AL'UMMA (CITAD) NA BAYAR DA HORO KAN ILIMIN NA'URA MAI KWAKWALWA***

## LABARAN CIKI




| | |
|---|---|
| **Muryar Matasa** | 1 |
| **Watch Dog** | 2 |
| **Ilimin 'Ya Mace** | 3 |
| Sharhin Yau da Kullum | 4 |
| **Shiri Na Mussamman** | 5 |
| **Siyasa Da Rayuwa** | 6 |
| **Ilimi Da Matasa** | 7 |



**Zaku iya sauraro da sauke manhajar CITAD RADIO ta wannan likau din dake kasa**



*https://play.google.com/store/apps/details?id=com.citad.org&hl=en&gl=US*

## CITAD Ta Buƙaci Gwamnati Da Ta Samar Hanyoyin Sadarwar a Yankuna Karkara

A ƙoƙarin da ta ke yi wajen an ganin samar da ingantattun hanyoyin sadarwa ga mutanen karkara da ƙauyuka, cibiyar bunƙasa fasahar da cigaban al'umma CITAD ta buƙaci gwamnatin tarayya da ta samar da hanyoyin sadarwar al'umma a yankunan karkara domin inganta fasaha a sassan Najeriya.

Babban daraktan cibiyar Yunusa Ya'u ne ya yi wannan kiran a jiya Talata a lokacin da ya ke jagorantar taron ganawa da manema labarai da ya gudana a ofishin cibiyar da ke Kano.



Malam Yunusa Ya'u ya ce cibiyar ta CITAD ya zama wajibi ta yi wannan kiran ga gwamnati akan samarwa da mutanen da su ke zaune a yankunan karkara hanyoyin sadarwa la'akari da irin yadda dokar kulle ta shafi rayuwar al'umma a lokacin annobar Korona.

## Matsalar tsaro: Yayin Da Iyaye Da Yan Uwan Daliban Jami'ar GFU ke Murna, A Jihar Neja Kwa Ƴan Bindiga Ne Suka Sace Mutane Sama da Dari a Jihar.

Mazauna wasu yankunan jihar Neja da ke tsakiyar Najeriya sun ce ƴan bindiga sun kai musu ƙazamin hari tare da garkuwa da mutane da dama a garin Shadaɗi.
Harin da aka kai a ranar Laraba na zuwa ne a daidai lokacin da matsalolin tsaro ke rincaɓewa a yankunan Neja tun bayan da gwamnan jihar ya tabbatar da cewa ƴan Boko Haram sun shiga garin.
Yanzu haka jama'ar garin Shadaɗi da ke karamar hukumar Mariga na cewa dubban mutane sun tsere bayan da ƴan bindigar suka kai masu hari.
Sannan akwai masu cewa waɗanda aka kashe sun haura mutum 100, adadin da gwamnatin jihar ta ce bai kai haka ba.

# DAGA YAN JARIDU
## Daga Buhari Abba

Ƙalubalen Da Yan Jarida Ke Fuskanta A Ƙasashe Masu Tasowa

Cin zarafi da kai hari kan ƴan jaridu don sun gudanar da aikinsu na zama daya daga cikin manyan kalubalen da ke fuskantar aikin jarida a kasashe masu tasowa kamar Najeriya, wanda ake ganin karuwarsa a sassa daban–daban na kasashen inda daga fadin gaskiya ko kuwa bankado zargi na aikata ba dai dai ba, ake kai musu hari, baya ga barazana ko kokarin rufe musu baki.

Akan haka ne gidan rediyon CITAD RADIO ya yi wata hira ta musamman akan wannan batun tare da mawallafin jaridar Nigerian Tracker , Malam Abbas Yusha'u Yusuf.

Ku saurari cikakkiyar hirar a shafin CITAD RADIO



## The Watch Dog
## Daga Gazzali Haruna Ibrahim

Shirin "The Wathc dog" shirine da ke maida hankali kan irin abubuwan da suke faruwa na cin hanci da rashwa da kuma tasirin su a cikin al'umma.

Shirin na gayyato masana, masu ruwa da tsaki, yan siyasa kan rawa da suke ganin da kuma tofa albarkacin bakinsu kan irin abubuwan da suke faruwa a yaki da cin hanci da rashawa.

Shirin na wannan makon ya karbi bakoncin Sameen Y Saeed, Executive Director, Youth Concerned Initiative akan Amfani da Ilimin Dabi'ar Dan Adam gurin infanta Ilimin 'Ya'Ya Mata.

.



## Ilimin 'Ya Mace
## Daga Gazzali Haruna Ibrahim

Shirin ilimin Ya mace shiri ne dake maida hankali kan abubuwan da suka shafi rayuwar ilimi musamman ma na mata , da hanyoyi da kuma dabaru



dan ganin an inganta ilim.

Shirin na karbar bakuncin matasa, mata masu fashin baki da dai sauransu.

Shirin Ilimin 'Ya Mace na wannan sati ya samu bakuncin Fa'iza Shehu, shugabar mujallar Telescope wadda muka tattauna da ita akan Hanyoyin Inganta Ilimin Mata a fanin Sana'oi.






## Sharhin Yau da Kullum Daga Ali Sabo

Sharhin Yau Da kullum Shirine da ke duba kan irin wainar da ake toyawa a duniya, sannan shirin na duba kan al'amuran yau da kullum na kasashen duniya.



Shirin na wannan makon ya karbi bakoncin Zubair A, Zubair, inda aka tattauna dashi akan Cikar Shugaban Amurka Kwana Dari, da kuma taron Kasashe masu tasowa guda bakwai da yanayin tsaro a yammacin Afrika.

Zaku iya saurara hirar ta www.citad.org/radio.



## Na Yi Farin Ciki Da Kokarin Da CITAD Ta Yi Akan Harkar Ruwan Sha A Ƙunchi - Aminu Idi Shuwaki

Na Yi Farin Ciki Da Ƙoƙarin Da CITAD Ta Yi Akan Harkar Ruwan Sha A Ƙunchi - Aminu Idi Shuwaki

Shugaban ƙaramar hukumar Ƙunchi a jihar Kano, Aminu Idi Shuwaki ya bayyana cewa ya yi matuƙar farin ciki da irin yadda jami'an Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa da Cigaban Al'umma CITAD, su ka yi akan batun ƙarancin ruwan sha da ake fama da shi a sassan yankunan ƙaramar hukumar.

Aminu Idi Shuwaki ya bayyana hakan ne a yau Alhamis a lokacin da ya ke tattaunawa da wakilan Cibiyar ta CITAD da kuma al'ummar ƙauyukan da su ke fuskantar matsalar ruwan sha a ofishin sa.

Shugaban ƙaramar hukumar ya ce daga lokacin da CITAD ta fitar da rahoton ƙarancin ruwan sha a yankunan kawo yanzu an samu kungiyoyi da ɗaiɗaikun mutane sun gina rijiyoyin burtsatse a yankunan da su ke fuskantar matsalar masu yawa.

Haka kuma ya ce a bisa wannan ƙoƙari da cibiyar CITAD ta yi, majalisar zartarwar ƙaramar hukumar Ƙunchi za ta aikowa da cibiyar takarda yabo ta musamman.

A nasa ɓangaren jami'an harkokin yaɗa labarai na cibiyar Ali Sabo, ya buƙaci shugaban ƙaramar hukumar da ya ba su haɗin kai wajen ganin an ga duk wanda ya dace domin samar da tsaftattccen ruwan sha a wadannan yankuna.

A ƙarshe shugaban ƙaramar hukumar ya bayar da tabbacin cewa a ko da yaushe a shirye ya ke wajen tunkarar dukkanin wanda ya ke da ruwa da tsaki wajen samar da ruwan sha a wadannan yankunan.

WWW.CITAD.ORG/
RADIO

Main Office:3rd Floor, NSITF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 080-68078282
080-54362931
070-33427467
E-mail: info@citad.org,
Website: www.citad.org

www.citad.org

Center For Information Technology and Development

**BABBAN EDITA**
Hamza Ibrahim

**EDITA**
Buhari Abba Rano

**MATAIMAKIN EDITA:**
Gazzzali Haruna Ibrahim

**MAI KULA DA TSARE-TSAREi:**
Ali Sabo

**Mai Kula Da Dab'i**
Salim Sani Shehu

AISHA SUFYAN UMAR

## GUZIRIN RAMADAN:

Yana daga cikin aqidar mabiya Sunnar Annabi (saw) (Ahlus Sunnah Waljama'ah) cewa, lallai Imani yana karuwa kuma yana raguwa, yana karuwa ne da ayyukan na gari, da'a kuma yana raguwa da ayyukan sabo da zunubai. Akwai Dalilai masu yawa da suke tabbatar da hakan.

**1-Dalili na farko:**
Fadin Allah Ta'ala a cikin Suratu Anfaal aya ta 2-4
"Abin sani Mumunai sune wadan da idan aka kirayi Allah, sai zukatansu su raurawa, kuma idan ana karanta musu ayoyin Allah sai Imanin su ya habaka/ karu, kuma ga Mahaliccinsu kadai suke dogara"
"Sune wadan da suke tsayar da sallah kuma daga abin da muka azurtasu suke ciyarwa"
"Irin wadan nan sune Muminai na gaske, suna da darajoji hawa hawa a wurin Mahaliccinsu da kuma gafara, da arziki mai karamci"

**2-Dalili na biyu:**
Fadin Allah ta'ala acikin, suratu Mudassir aya ta 31.
"Bamu sanya ma'abota (masu gadin) gidan wuta ba face Mala'iku, kuma bamu sanya adadinsu ba face don ya zama fitina ga wa□anda suka kafirta, domin kuma wadan muka baiwa littattafai su kara samun yakini kuma domin mu habakar/kara ma wadan da su kayi Imani da wani Imanin....".

**ABUBUWA GUDA GOMA-5 SUNA KARA IMANI**

Yaku yan'uwana mu sani lallai Imani yana karuwa kuma yana raguwa,yana karuwane da karuwar wadansu aiyuka guda goma,kuma yana raguwa da raguwar aiyukan guda goma gasu kamar haka:
1-Sanin Allah madaukakin sarki,da sanin Sunayansa mafiya kyau da siffofinsa madaukaka.
Allah yana cewa:
( ٢٨ : إنما يخشى الله من عباده العلماء ( فاطر
Lallai Malami sune sukafi kowa sanin Allah da sunayansa da siffofinsa, sai suke yawaita ambatan sunayansa da siffofinsa wajan Addu'oinsu da sauran ibadunsa har hakan ya sanya masu jin tsoransa Allah,wanda dashine imani yake karuwa.
ابن رجبAllah yayi masa rahama yana cewa:
"Ilimi mai amfani ya kunshi abubuwa guda biyu:
A-Sanin Allah Ta hanyar sanin sunayansa da siffofinsa madaukaka,da kuma kokarin sanin ma'anoni-su da aiki dasu ta yadda hakan zai sanyama bawa jin tsoran Allah da kuma kwadayin rahamarsa da dogaro dashi da kuma koma zuwa gareshi.
B-Sanin abinda Allah yake so kuma ya yardashi wanda dashine ake bauta masa,da kuma sani abinda Allah baya so kuma yake fusata Allah da kuma kuje masa.
@ ) 65-64 ( فضل علم السلف على فضل الخلف في ص
-2Neman ilimin shari'a wanda shine kadai tsani da zai kai mutum samun sannin Allah da jin tsoransa wanda hakan zai sanya ya samu karfin imani.
3-Yin dubi da Nazari akan ayoyin Allah na halitta da kuma dubi akan halittun Allah madaukakin sarki.
Allah yana cewa:
إن في خلق السموات والأرض واختلاف الليل والنهار لآيات لأولي الألباب { عمران : ١٩٠
وفي أنفسكم أفلا تبصرون { الذاريات :
قل انظروا ماذا في السموات والأرض وما تغني الآيات والنذر عن قوم لا يؤمنون { يونس : ١٠١
Amir Bin Abdil qais yana cewa:
"Naji sama da mutum ukku daga cikin Sahabban Annabi s.a.w suna cewa:
"Lallai karuwar Imani ko hasken imani yana cikin tunani akan ayoyin Allah"
@ ) 2/409 انظر الدرر المنثور
-4Yawaita karatun alqurani da kuma kokarin sanin ma'anoninsa da dubi acikin hikimominsa.
Allah ya bamu labarin muminai na gaskiya,sai yace:
} ٢ : وإذا تليت عليهم آياته زادتهم إيمانا [} الأنفال
: أفلا يتدبرون القرآن أم على قلوب أقفالها { محمد :
Ibn Qaiyim Allah yayi masa rahama yana cewa:
"Karanta aya daya tare da yin tadabbirinta da kokarin gano ma'anarsa,yafi sauke alqurani batare da yin tadabbirun ayoyinsa ba, domin yin tadabburi acikin ayoyin alqurani mai girma yana sanya zuciya ta sami karuwar imani da zaqin karanta alqurani"
@ 1/485 انظر مدارج السالكين
-5Yawaita Ambaton Allah.
Allah yana cewa:
الذين آمنوا وتطمئن قلوبهم بذكر الله ألا بذكر الله تطمئن
القلوب { الرعد :
Da kuma fadin Annabi s.a.w:
(Misalin wanda yake ambaton Allah da wanda baya ambatonsa kamar misalin rayayyene da matacce)
@Bukhari
Ambaton Allah shine rayuwar zuciya da imani da kuma karuwar imani a duk lokacin da ya yawaita ambaton Allah,mutuwar zuciya da kuma raguwar imani yana faruwane duk lokacin da bawa yayi nisa da ambaton Allah.
أبو الدرداء رضي الله عنهyana cewa:
"Yana daga cikin alamun Allah buwayi ya kar□i azumin mai azumi shine bayan azumin ya wuce sai shima ya ci gaba da aikata kyawawan aiyuka nagari kamar yadda ya kasance yana aikatawa acikin watan azumin ko makamancin hakan, bawai sai bayan Ramadana ya wuce sai shima ya koma kan mu-nanan halayensa ba"
-
"Alamu ne na ta□ewa da kuma rashin nasara ga rayuwar wanda bayan watan Ramadana ya wuce sai kaga ya koma yana aikata abinda ya kasance yana aikatawa marasa kyau"
-
"Shi watan Ramadana wata ne neman yafiyar Allah, da kuma samun □a'nci daga wuta, ana so bayan ya wuce ka □ora kyawawan aiyuka nagari kamar yadda kake aikatawa acikinsa ko kuma makamancin hakan"